# Duk wanda ya farar da wani abu a cikin wannan Addinin namu wanda ba ya ciki, to shi abun mayarwa ne

Daga uwar muminai Babar Abdullahi Nana A'isha - Allah Ya yarda da ita -, ta ce: Manzon Allah - tsira amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: «Duk wanda ya farar da wani abu a cikin wannan Addinin namu wanda ba ya ciki, to shi abun mayarwa ne». A cikin wata riwaya ta Muslim: «Wanda ya aikata wani aikin da babu umarninmu a cikinsa to shi abin mayarwa ne».

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana bayyana cewa wanda ya yi kirkira a Addini ko ya aikata wani aikin da wani dalili bai yi nuni akansa ba na Alkur’ani ko hadisi, to shi abin juyarwane akan mai shi ba abin karba ba ne a wurin Allah.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee